# TARBIYYA A SHARI'AR MUSULUNCI

NA:
ABU-ABDILLAH
ALIYU IBRAHIM MUHAMMAD
(ALMAJIRI ALKAFAWEE)

BITA:
IMAM DR. AHMAD RUFA'I NASIR

# TARBIYYA A SHARI'AR MUSULUNCI

NA:
ABU-ABDILLAH
ALIYU IBRAHIM MUHAMMAD
(ALMAJIRI ALKAFAWEE)

**Gabatarwa:**

Godiya sun tabbata ga Allah wanda ya ni'imta mu da ƴaƴa kuma ya sanya su ƙawa da kwalliya garemu a wannan rayuwar, Allah maɗaukakin sarki ya na cewa: ﴿**Dukiya da yaya su ne kwalliyar rayuwar Duniya**﴾ **Al-Kahfi:46**. Kuma ya sake cewa: ﴿**Kuma Allah ya sanya muku daga gare ku mataye, kuma ya sanya muku daga matayen ƴaƴa da jikoki, kuma ya azurta ku daga daɗaɗan abubuwa**﴾ **An-Nahl: 72.**

Na shaida babu abun bauta bisa cancanta sai Allah shi kaɗai ba shi da abokin tarayya wanda ya gargaɗe mu kuma ya ja mana kunne daga fitinar ƴaƴa a inda yace: ﴿**Lallai daga matayen ku da ƴaƴan ku akwai maƙiyi a gare ku**﴾. **Al-Tagabun: 14** Kuma yace: ﴿**Lallai Dukiyoyin ku da ƴaƴan ku fitinace**﴾. **At-Tagabun: 15.**

Allah ya yi mana gargaɗi game da abu kuma ya koya mana yadda za mu mu'amalanci wannan abun, ya shar'anta mana a harshen manzonsa صلى الله عليه وسلم hukunce-hukunce, da sunnoni da wajibai da suke da alaƙa da ƙananan yara kamar kaciya da aƙiƙah (yanka ranar bakwai) da koyar da su sallah da waninsa, kuma ya gargaɗe mu game da son ƴaƴa da zai kai ga wuce iyakar

Allah ko mu gabatar da abun da ɣaɣa su ke so akan abun da Allah yake so.

Saboda da yawa daga cikin mutani sun jahilci abun da ke da alaƙa da mu'amala da ɣaɣa (tarbiyya) musammam waɗanda ba su da alaƙa da karance-karancen littafan larabci, sai na tattaro a taƙaice wasu mahimmam abubuwa da su ke da alaƙa da wannan daga Qur'ani da Sunnah da fahimtar malamai magabata na kwarai da na zamani don mu gudu tare mu tsira tare.

Allah na ke roƙo da ya sanya wannan aiki ya zama don neman yardar shi kuma ya amfanar da musulunci da musulmai kuma ya amfanar da ni da wannan aiki duniya da lahira.

وصلى الله وسلم على نبينا محمد وعلى آله وصحبه أجمعين

**Abu-Abdillah Aliyu Ibrahim Muhammad**

***(Al-Majiri Al-Kafawee)***

## MUHIMMANCIN TARBIYYAH

Akwai buƙatar sanin muhimmancin tarbiyya domin fahimtar girman sa.

Za mu fahimci muhimmancin ta ta hanyoyi kamar haka:-

**<u>Hanya Ta Farko:</u>**

Tsayuwar da annabawa da manzonni صلوات الله وسلامه عليهم su ka yi wajan tarbiyyan ɣaɣan su:

1. **<u>Annabi Nuuh [عليه السلام]</u>**

Allah [سبحانه وتعالى] ya na faɗa a ƙissar Annabi Nuuh (A.S) tare da ɗansa: ﴿...**sai Nuh ya kirayi ɗansa alhali kuma ya kasance can wuri mai nisa. Ya ƙaramin ɗa na! Zo ka hau tare da mu, kuma kada ka kasance tare da kafirai) Ya ce: "Zan tattara zuwa ga wani dutse ya tsare ni daga ruwan". (Nuhu Ya ce, "Babu mai tsarewa a yau daga umarnin Allah face wanda ya yi ma rahama". Sai taguwar ruwa ta shamakance a tsakanin su, sai ya kasance daga waɗanda aka nutsar**﴾**. Hud: 42-43.**

﴾**Kaga duk da Allah ya sanar da shi cewa babu wanda zai ƙara Imani daga mutaninka**﴿, **(Hud: 36)** amma bai fid da tsammani daga ɗansa ba.

2. **Annabi Ibrahim [عليه السلام]:**

a-Allah [سبحانه وتعالى] yace: Ɗ**Kuma a lokacin da ubangijin Ibrahim Ya jarabe shi da wasu kalmomi, sai ya cika suɗ**. Ya ce:

﴾"**Lalle ne Ni, mai sanya ka shugaba domin mutane ne, yace: "Kuma daga zuriyata." Yace: "AlkawariNa ba zai samu azzalumai ba**"﴿ **Baqara: 125**

b. Allah [سبحانه وتعالى] ya sake cewa: Ɗ**Kuma a lokacin da Ibrahim yake daukaka harsashin gini ga 'Dakin, da Isma'ila (Suna cewa) "Ya Ubangiji! Ka karɓa daga gare mu, lalle ne kai, kai ne mai ji, Mai Sani (127) "Ya Ubangijinmu Ka sanya mu mu biyu, waɗanda suka sallama (al'amari) gare ka, kuma daga zuriyarmu (Ka sanya) al'umma mai sallamawa zuwa gare ka, kuma ka nuna mana wuraren ibadar hajjinmu, kuma ka karbi tuba a kanmu, lalle ne kai, kai ne mai karɓar tuba, mai rahama (128) ya ubangijimu ka aiko, a cikinsu, wani manzo daga garesu, yana karanta musu ayoyinka, kuma yana**

**karantar da su littafin da hikimar, kuma yana tsarkake su. Lalle ne kai ne Mabuwayi Mai Hikima (129)**].

"A cikin waɗannan ayoyi, a kwai shar'antuwar rokan Allah a kan kanka da kuma zuriya tabbatuwa a kan musulunci har mutuwa". **[Duba Littafin:(أيسر التفاسير) na Al-jaza'iriy]**

**Tsokaci:**

Kuma muhimmancin koyawa ƴaƴa tuba da miƙa al'amura zuwa ga Allah dan babu makawa sai mutum yayi ba dedeba dan shi mai kuskure ne.

3. **Annabi Ya'qub [عليه السلام]:**

Allah [سبحانه وتعالى] yace: ﴿**Ko kun kasance halarce a lokacin da mutuwa ta halarci Ya'akubu, lokacin da yace wa ƴaƴansa: "Mene ne za ku bauta wa daga bayana?" Suka ce: "Muna bauta wa Abin bautawarka kuma Abin bautawar iyayenka Ibrahim da Isma'ila da Is'haƙa, Ubangiji Guda, kuma mu a gare shi masu sallamawa ne"**﴾. **Baqarah: 133.**

"A cikin ayar akwai muhimmancin wasiyya ga ƴaƴa da sauran iyalai da riƙe musulunci har su mutu a kai". **[Duba Littafin:(أيسر التفاسير) na Al-jaza'iriy]**

**Hanya ta Biyu:**

Kwaɗaitarwan da Annabi [صلى الله عليه وسلم] ya yi a kan kula da tarbiyya;

a. An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar R.A, daga Annabi صلى الله عليه وسلم yace: ((**Dukkan ku makiyaye ne, kuma dukkan ku abin tambaya ne game da abun da aka ba shi kiwo...**)) **Bukharee: 5188 da Muslim: 1829**

b. An karɓo daga Abu-Hurira-R.A lallai manzon Allah صلى الله عليه وسلم yace: ((**Idan ɗan Adam ya mutu dukkan ayyukansa sun yanke sai dai gudu uku: Sadaƙa mai gudana, ko ilimi da a ke amfana da shi, ko ɗa nagari da ya ke yi masa addu'a**)) **Muslim:1631**

c. An karɓo daga Abu-Hurairah R.A daga Annabi صلى الله عليه وسلم yace ((**Lallai mutum ana ɗaga darajar sa a Al-Jannah sai yace: daga ina wannan darajar? Sai ace: saboda addu'ar ɗanka gareka**)). **Ibn Majah: 3660**

## Ƴaƴa Ni'ima ne Daga Allah kuma kyauta ne

Abun da a ke nufi da kyauta: Shine a ba ka ba tare da ka biya ba ko ta wata hanya.

Allah [سبحانه وتعالى] yace: ﴿**Mulkin sammai da ƙasa na Allah ne kawai, Yaa halitta abin da yake so. Yana bayar da ɥaɥa mata ga wanda yake so, kuma yana bayar da ɥaɥa maza ga wanda yake so (49) ko kuma ya haɗa su maza da mata, kuma yana sanya wanda ya so bakarare lalle Shi, Mai ilimi ne, Mai ikon yi (50)**.﴾

**Ash-Shura:29-50**

"Ayoyin nan suna cewa Allah ne kaɗai mai tasarrufi a duniya gabaɗaya kuma shine mai bayarwa kuma mai hanawa don wata hikima mai girma wacce hankalin bayi ba zai iya hankaltowa ba"

**[Duba Littafin:(أيسر التفاسير) na Al-jaza'iriy]**

## Matakan Tarbiyya[1]

Saboda muhimmanci wannan amanar (ƴaƴa) da girman sa zan ambaci wasu matakai daga mafi muhimman matakai da kuma tushe (asasi) da ya kamata kowani uba ya lura da shi saboda ya samu nasarar abin da ya ke nema:

1. **Zaɓen Abokiyar/Abokin Zama**

   Lalle daga mafi girman matakan tarbiyyah, Zaɓen abokiyar zama ta gari, kuma wannan ya na kasancewa ne kafin a haihu saboda za ta zama mai taimakawa wajen tarbiyyar su da ladabtar da su.

   Saboda haka ne ma kwaɗaitarwa ya zo daga manzon mu صلى الله عليه وسلم a kan zaɓen mace ma'abociyar addini kamar yadda hadithi mai lamba 5090 a Bukharee da 1466 a muslim.

2. **Addu'a**

   Daga mafi muhimmacin matakan tarbiyya akwai addu'a ga ƴaƴa, kuma wannan addu'ar zai kasance ne kafin zuwan ƴaƴan, da kuma bayan zuwan ƴaƴan.

---

١ ركائز في تربية الأبناء للشيخ عبد الرزاق البدر

Ga matakan addu’ar kamar haka:

a. ***Addu’ar neman zaɓin Allah a kan wacce mutum ya ke so ya aura***:

Jabir ɗan Abdullahi رضي الله عنه ya ke cewa! “Manzon Allah صلى الله عليه وسلم ya kasance ya na karantar da mu neman mafi alkairi (Istikhara) a dukkan al’amura kamar yadda yake karantar da mu sura daga Kur’ani” **Bukharee: 1162**

b. ***Addu’a a yayin saduwa***

Ya tabbata daga Annabi صلى الله عليه وسلم yace: ((**Da ɗayan ku in ya yi nufin saduwa da iyalin sa yace:” Da sunan Allah, Allah ka nisantar da sheɗan daga garemu kuma ka nesantar da sheɗan daga abun da ka azurta mu shi”, in a ka ƙaddara ɗa tsakanin su a wannan saduwar to, sheɗan ba zai cutar da shi ba har abada**)[1]

c. ***Addu’a bayan haihuwa***

Iyaye za su yi ma ƴaƴan su addu’ar shiriya bayan haihuwa da neman su tabbatu a addini don yin hakan koyi ne da annabawa kamar annabi Ibrahim عليه السلام[2] da kuma bayin

---

[1] Bukharee: 3271
[1] Ibrahim: 35-41

Allah mai rahama da Allah ya yi bayanin su a cikin Al-ƙur'ani (1) da kuma hadithin da ya tabbata manzon Allah صلى الله عليه وسلم yace: ((**Addu'a guda uku karɓaɓɓu ne babu shakka ko kokonto a ciki: Addu'ar uba ga ɗansa, addu'ar matafiyi, Addu'ar wanda a ka zalunta**))[2]

3. **Zaɓen Suna Mai kyau**

Daga cikin haƙƙoƙin ɗa a kan mahaifi akwai kyautata masa suna kamar yadda ya inganta daga Annabi صلى الله عليه وسلم: ((**Lallai mafi soyuwan sunayen ku a wajen Allah: Abdullahi da Abdurrahman**)).[3]

Haka kuma annabi صلى الله عليه وسلم yace: ((**Lallai ku za'a kira ku a ranar Alƙiyama da sunayen ku da kuma sunayen iyayen, saboda haka ku kyautata sunayenku**)).[4]

Akwai wasu daga cikin sahabbai waɗanda annabi صلى الله عليه وسلم ya canza musu sunaye saboda sunan da iyayen su suka sanya musu bai dace ba, kamar "Zainab", asalin

---

[2] Al-Furqan:74
[3] Abu-Dawud, Tirmidhee:1905
[4] Muslim:2132
[5] Abu-Dawud:4948

sunanta "**Birrah**" sai Annabi ya canza[1], kamar "Juwairiyya" ita ma asalin sunan ta "**Birrah**".[2]

Haka kuma ya na da muhimmanci sanya wa ƴaƴa al-kunya (Abu-wane ko Ummu-Wance).

Sayyiduna Umar رضي الله عنه ya na cewa: (**Ku gaggauta sanya wa ƴaƴan ku alkunya tun kafin alkunya marasa kyau su rigaye ku**)).[3]

4. ***<u>Nasiha da sanya masu Manufa (Goal)</u>***

Dogewa a kan yi musu Naseeha da basu mafuskanta musamman a kan ɗabi'u na karamci kamar dasa masa Aƙida na Addini a farillan Musulunci, da rukunan Musulunci da sauran al'amuran shari'ah. Haka wajan yi musu faɗa da tsawatarwa, mutum ya fara musu da manyan zunubai sa'annan sauran abubuwan da shara'a ta hana, waɗannan suna da kaso mai tsoka wajen mafuskantar su.

---

[6] Bukaree:6190
[7] Fath: 1/705
[8] Al-Adaabus-shariyyah Na Ibn Muflih

## 5. <u>Ka/Ki Zama Abun koyi Gare Su</u>

Daga cikin matakan tarbiyya mai girma: Shine iyaye su zama abun koyin ƴaƴan su, in ya umurce su da wani abu to ya zama a gaba wajan aikatawa, in kuma ya hana su to, ya zama a gaba wajan bari, kar ya zama maganganun sa su saɓa ma aikin sa, mu rinƙa hararo maganar Allah da ya ke zargin Baniy Isra'ila inda ya ke cewa: ((**Shin, kuna umurnin mutane da alheri, kuma ku manta da kanku alhali kuwa kuna karatun littafi? Shin ba za ku hankala ba?**)). **Baqarah: 44**

Da maganar da Annabi Shu'aibu صلى الله عليه وسلم ya yi ma mutanin sa ya ke cewa: ((...**Kuma ba ni nufin in saɓa muku zuwa ga abun da nake hana ku daga gare shi...**)). **Hud: 88**

Da kuma faɗin Allah سبحانه وتعالى: ((**Yà kú waɗanda suka yi imàni! Don me kuke faɗin abin da bà ku aikatawa (2) ya girma ga zama abun ƙyama a wurin Allah, ku faɗi abin da bà ku aikatawa** (3))) **Saff: 2-3**

Malamai su na cewa "***Karantarwa a aikace ta fi tasiri sama da karantarwa da baki***".

## YIN AMFANI DA ƘARFI WAJAN TARBIYYA DA LADABTARWA

Babu shakka cewa yin amfani da tausayi da tausasawa ya na da cikin mafi muhimmancin uslubin tarbiyya, kuma Annab ﷺ ya kasance ya na aikata hakan.

Amma idan wannan bai yi amfani ba, to lallai hikima ita ce sanya abu a bigiren shi da dabara da kuma ƙwarewa ba tare ƙari ko ragi ba da sharaɗin lazimtar sharaɗin da dokokin Shari'ah.

Haƙiƙa nassoshin Shari'a sun tabbatar da yin amfani da ƙarfi wajen tarbiyya a lokacin da buƙatar hakan ta taso.

Ga wasu daga nassoshin da su ke magana a kan sharuɗɗan amfani da ƙarfi wajen tarbiyyah:

1. Annabi ﷺ ya yi hani game da duka a fuska; a Hadisin da aka karɓo daga Abu-Huraira رضي الله عنه a cikin Sahihu Muslim: 2612.

2. Annabi ﷺ ya hana yin duka kamar a na dukan bawa a Hadisin da a ka karɓo Daga Abdullahi ɗan Zam'ah رضي الله عنه a cikin Sahihul-Bukhariy: 6042 da Muslim: 2855ɗ

3. Annabi ﷺ ya yi umurni da a canza mummuna zuwa kyakkyawa da hannu a Hadisin da a ka karɓo daga Abu-Sa'id Al-Khudriy R.A a cikin ƊSahihu Muslim: 49ɗ

4. Annabi ﷺ ya yi umarni da a daki yara in sun kai shekaru goma ba su Sallah a Hadisin da karɓo Amru ɗan Shu'aibu daga babansa daga kakarsa رضي الله عنه, a cikin Sunanu Abi-Dawud: 494.

5. Annabi ﷺ ya yi hani a kan bulala sama da goma sai dai a haddi daga haddodin Allah, a hadithin da a ka karɓo daga Abu-Burdah رضي الله عنه a cikin Sahihul-Bukhariy: 6848 da Sahihu Muslim: 1708.

6. Annabi ﷺ ya yi umurni da rataya bulala a inda Mutanin gida za su dunga gani a Hadisin da a ka karɓo daga Ibn Abbas رضي الله عنه cikin ƊMu'jam na Aɗ-ɗabaràniy kuma Imamul Albaniy ya Hassana a cikin As-Sahīhah: 3/432.

Duka Hadisai da suka gabata suna bayani ne na sharuɗɗn amfani da ƙarfi wajen tarbiyya.

<u>FALALAR TARBIYYAR ƳAƳA MATA</u>

Abun baƙin ciki ne matuƙa a ce har yanzu akwai waɗanda in aka haifa musu ƴaƴa Mata suna shiga baƙin ciki, amma wannan aikin ya na daga cikin ayyukan Jahiliyyar farko da Allah ya zarge su a kan haka a Suratul-Nahl: 58-59.

Musulunci ya Sanya tarbiyyan ƴaƴa mata daga hanyoyin samun Al-jannah:

i. An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi رضي الله عنه yace: "Na ji Manzon Allah ﷺ yana cewa: ((**Duk wanda ya ke da ƴaƴa mata guda uku kuma ya kula da su, ya tausaya musu, ya ɗauki ɗawainiyarsu, ya aurar da su, to Aljannah ta wajaba masa**))[1]

ii. An karɓo daga Anas ɗan Malik رضي الله عنه, Lallai Manzon Allah ﷺ yace: ((**Duk wanda ya yi hidima ma ƴan mata biyu har suka girma zai zo ranar Alƙiyamah ni da shi, sai ya haɗa ƴan yatsunsa ﷺ**)).[2]

iii. An Karɓo daga ɗan Abbas رضي عنهما yace: Manzon Allah ﷺ yace: ((**Duk wanda yake da ƴa Mace bai kashe ta tana ƙarama**

[1] Musnadu Imami Ahmad:14247
[2] Muslim:2631

**ba, bai wulaƙanta ta ba, bai fifita ƴaƴansa maza a kan ta ba, Allah zai shigar da shi Aljannah**)).[1]

[1] Abu-Dawud:5146

**RUFEWA:**

Ina roƙon Allah da Ya gyara mana niyya gabaɗayanmu da zuriyanmu, Ya gafarta ma iyayenmu, kuma Ya saka musu da mafificin Alheri.

Ina roƙon Allah da Ya taimake mu a kan tarbiyyar ƴaƴanmu a kan Al-Ƙur'ani da Sunnah, kuma Ya sanya su zuri'a ta gari, kuma su zama mana sanyin idanu a duniya da lahira.

Ina roƙolon Allah da Ya sakawa Malumanmu, Ya gafarta ma waɗanda suka mutu daga cikin su.

***Salati da Aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammad, ﷺ da Iyalansa, da Sahabbansa gabakiɗaya.***

***Abu-Abdillah Aliyu Ibrahim Muhammad***
***(Al-Majiri Al-Kafawiy)***
***13-Safar, 1445***
***30-August, 2023.***



# TARBIYYA A SHARI'AR MUSULUNCI